

Kicchu ya farka da sassafe.  yana hamma, saiyace "Lokacin kama kifiya yi,".



Ya hadu da Choru akan hanyar zuwa tafki don kamun kifi.
Sun kasance abokan juna,
Saboda shakuwarsu da juna, tare suke wasa, suke komai duk tsawon rana.



Munia ta gansu dauke da fatsarsu kan hanyarsu ta zuwa kamun kifi.

Munia karama ce, sai ta yi tunani, tace, "Don Allah kada kuyi kamun kifi," saboda, "In ba ruwa, kifi ba zai rayuba."



Ba su ko saurari abin da Munia take fada ba. Sai suka ka nufi tafkin kai tsaye.



Kicchu da Choru suna zaune a bakin tafki suna jira.Sai ga Kifaye biyu suna iyo a cikin ruwa, daya siriri dayan kuma zagayayye.




Can sai ga kifi na uku, mafi girma da suka gani. Sai Munia ta yi dariya, tace " Wannan Ya fi girman kafafun Appa!"




Kicchu da Choru sun rike fatsarsu sossai.



Kichu ya ja fatsar sossai
Shi ma Choru ya ja da karfi sossai



BAAATTT! Sai fatsar su ta karye.
DUUUUM! Kicchu ya fadi kasa.
TANDAM! Sai Choru ya fada cikin ruwa.







Ko kun san menene ya faru?

Me kuke tunani?

Kifi ne ya harde igiyoyin fatsar!

